## GYARTAI

*Gyar̃tai yanà gyāran sauyà.*

**Abdùllāhì:** Sàlāmù àlaikùm.

**Gyar̃tai:** Wà àlaikùm às-sàlâm.

**A:** Ìnā wunì?

**G:** Lāfiyà lau.

**A:** Ìnā gàjiyà?

**G:** Lāfiyà lau.

**A:** Don Allàh gà ƙwaryātā zā à ɗinkè.

**G:** Tô.

**A:** Nawà zā à biyā?

**G:** Nawà zā kà biyā?

**A:** Kai zā kà fàɗā.

**G:** Kàwō Nair̃à bìyar̃.

**A:** Nair̃à bìyar̃ wannàn?

**G:** Ī.

**A:** Nair̃à ukù.

**G:** Ā'à, àlbar̃kà.

**A:** Nair̃à huɗu.

**G:** Tô kàwō kuɗī.

**A:** Tò mādàllā. À ɗinkè.

*Yā fārà ɗinkàwā.*

**A:** Tô yàyà bā kà hūdàwā dà ... Dà mè akè hūdàwā nè?

**G:** Kibiyà, kā gan tà.

**A:** Tò kà kūnà kuma kà hūdà ta kō? Tò kà hūdà, kàmar̃ kanà hūdàwā. *Gyar̃tai yā hūdà.* Yâuwa.

*Gyar̃tai yā ci gàba dà ɗinkì.*

**A:** Tò̄ mɛ̀nē nɛ̀ sūnan wannàn? *Yā nūnà sauyà̄.* Wannàn.

**G:** Wannàn?

**A:** Ē.

**G:** Sauyàr̃ kabà̄.

**A:** Sauyà̄?

**G:** Ē.

**A:** Sauyàn kabà̄?

**G:** Sauyà̄.

**A:** Sabyà̄?

**G:** Sauyà̄.

**A:** Tò̄ sauyàr̃ kabà̄?

**G:** Ē.

**A:** Ē tò̄ nā gānè̄. Wancàn shī nè̄ kùr̃tū?

**G:** Ē, wannàn ba. *Yā nūnà̄ kùr̃tū.*

**A:** Ē.

**G:** Ē.

**A:** Mè̄nē nè̄ à cikin kùr̃tûn?

**G:** Kāyan ɗinkìn nē [tô] na wannàn ɗin nè̄ wannàn.

**A:** Dà ruwā dà sauyà̄?

**G:** Ē.

**A:** Tò̄ mādàllā.

*Yā ci gàba dà ɗinkì̄.*